**KA'IDOJIN DA AKA SHIN FIDA NA AIKI AKAN JIMA'I GA MA'AIKATAN AGAJI**

Za'a iya ladabtar da ma'aikatan Agaji, koma a kore su idan suka jefa kansu cikin jima'i ta hanyar da bata
Dace ba. Ga ka'idojin da dole zasu lura da su: domin yin aiki dasu Misali Kamar Haka.

- Ba'a yarda ma'aikatan Agaji suyi amfani da duk wacce take kasa da shekara 18 ba, koda kuwa hakan dai dai ne a kasarsu. Fadar cewa basu san ainihin shekarun wadda suka Nema ba, bazai zama hujja ba a garesuba.

- Ba'a yarda ma'aikatan A gaji su biya kudi domin saduwa da mace ba, ko samun aiki, ko sayen wasu kaya, ko wata kulawa da aka tanada Na musamman saboda mabukata. Kada su taba yiwa wasu alkawarin sama musu wadannan abubuwa domin biyan bukatar kansu da zata muzgunawa mabukatan. Wannan kuma ya hada da biya ko bada kudi a yi amfani da mai zaman kanta. Yin hakan zai iya karya dokan aikin Agaji.

- Ma'aikatan Agaji ne suke da damar samar da kayayyaki da abubuwan bukata. Hakan ya saka suna da karfi fiye da mabukatan da suke neman taimako. Saboda wannan dalilin, kungiyoyin bada Agaji suka karfafa cewa le. llai kada ma'aikatansu su sake su nemi wata mace wacce take bukatar Agajin gaggawa. Saboda irin wannan dangartakar takan gurbata aikin Agaji da rashin gaskiya da amana.

- Idan wani daga cikin ma'aikatan agaji ya damu cewa, yana zargin wani daga cikin ma'aikacinsu ko na wata kungiyar agajin daban yana karya dokokin aikin agaji akan jima'i, dole ya bada rahoto ta hanyar ka'idojin bada rahoton kungiyarsu.

- Dole ne ma'aikatan agaji su tabbatar da sun samar da wajen aiki mai tsafta da zai kare Abubuwan da ki game da jima'i, kuma karfafawa ma'aikata kwarin gwiwar bin ka'idojin aiki. Dukkan shugabanni su suke da alhaki da kuma bunkasa wadannan hanyoyi domin samar da yanayin da ya dace.

Zaku sami ka'idojin IASC na cutarwa da muzgunawa ta hanyar lalata anan: http://www.pseataskforce.org/uploads/tools/sixcoreprinciplesrelatingtosea iasc english.doc.
Wannan daftarin an samar da shi ne da hadin gwiwar IASC Task Team on Accountability to

Affected Populations da Protection from Sexual Exploitation and Abuse da kuma Translators without Borders.